# Me Ya Kamata Ka Yi?

Ka ɗan rubuta amsarka ga kowace tambaya a sararin da aka samar. Ka sanya a ranka babu amsoshin da ba daidai ba. Ka ɗan yi tunani a natse game da tambayoyin sannan ka raba naka ra'ayin.

## Labari na 1

Sofia da aminiyarta Joaquín sun yi faɗa. Bayan nan, Sofia ta raba wani aiken mugunta game da Joaquín a dandalin sadarwar zamani. Daga baya a wannan daren, Joaquín ta aika mata da sako sannan suka yafe wa juna, amma duk da haka aikenta yana nan a intanet.

- Mene ne zai iya faruwa?
- Me ya kamata Sofia ta yi? Me ya kamata Joaquin ta yi?
- Shin za ka iya tuna wani misalin irin wannan yanayin da ya faru a rayuwa?

## Labari na 2

David ya ɗauki hotunan wasu daga cikin abokansa da suke yin wasu abubuwan sakarci kuma ya aike da su a dandalin sadarwar zamani, tare da alamar hash da zai iya zama rashin ladabi ko mugunta, amma duk a cikin wasa tare da abokansa. Kashegari, Ctalina, wata ƙawar, ta zo wajen shi a makaranta ta ce ta zata cewa alamar hash ɗin yana da cutarwa sosai da kuma nuna jima'i (ma'ana., ra'ayi ko nuna bambanci bisa ga jinsi; musamman nuna bambanci a tsakanin mata).

- Mene ne zai iya faruwa?
- Me ya kamata David ya yi? Me kuma ya kamata Catalina ta yi?
- Idan fa Catalina ta tuntuɓi David ta intanet a maimakon ido da ido?
- Shin za ka iya tuna wani misalin irin wannan yanayin da ya faru a rayuwa?
- Idan fa Catalina ta fara kiransa mai cutarwa? Yaya kake ganin idan aka kalli mutum a matsayin mai zalunci zai shafi sunan David a nan gaba?

## Labari na 3

Aditi tana kan dandalin sadatwar zamani a lokacin da ta lura cewa Mary, wata yarinya a makaranta, ta ɗauki hotonta sannan ta rubuta, "haha #menenebazaasanyaba" (yi ma suturarta dariya). Lallai, Aditi ta hassala sosai.

- Mene zai faru?

- Me Ya Kamata Mary Ta Yi? Me ya kamata Aditi ta yi?

# Me Ya Kamata Ka Yi? Kwafin Mai Karantarwa

Ka ɗan rubuta amsarka ga kowace tambaya a sararin da aka samar. Ka sanya a ranka babu amsoshin da ba daidai ba. Ka ɗan yi tunani a natse game da tambayoyin sannan ka raba naka ra'ayin.

## Labari na 1

Sofía da aminiyarta Joaquín sun yi faɗa. Bayan nan, Sofia ta raba wani aiken mugunta game da Joaquín a dandalin sadarwar zamani. Daga baya a wannan daren, Joaquín ta aika mata da sako sannan suka yafe wa juna, amma duk da haka aikenta yana nan a intanet.

- Mene ne zai iya faruwa?
- Me ya kamata Sofia ta yi? Me ya kamata Joaquin ta yi?

Wani zai iya ganin aiken sannan ka kai ƙarar Sofia soboda cin zali ko yi mata mummunar fahimta da dangantakar Joaquín da yanda suke ji a tsakanin juna. Duk da haka Joaquín zai iya ganin aiken a matsayin rashin ladabi. Zai iya zama ra'ayi mai kyau ga Sofia domin ta cire aikenta.

- Shin za ka iya tuna wani misalin irin wannan yanayin da ya faru a rayuwa?

Ya kamata a nuna mahalarta taron a misalan da suka fuskanta ko suka ji labari a baya. Ka sanya a ranka cewa raba waɗannan misalan na zahiri a rayuwa zai iya kasancewa rashin samun natsuwa ga mahalarta taron. Ba su damar raba misalan abokai ko mutanen da suka sani (da. kansu).

## Labari na 2

David ya ɗauki hotunan wasu daga cikin abokansa da suke yin wasu abubuwan sakarci kuma ya aike da su a dandalin sadarwar zamani, tare da alamar hash da zai iya zama rashin ladabi ko mugunta, amma duk a cikin wasa ne tare da abokansa. Kashegari, Ctalina, wata ƙawar, ta zo wajen shi a makaranta ta ce ta zata cewa alamar hash ɗin yana da cutarwa sosai da kuma nuna jima'i (ma'ana., ra'ayi ko nuna bambanci bisa ga jinsi; musamman nuna bambanci a tsakanin mata).

- Mene ne zai iya faruwa?
- Me ya kamata David ya yi? Me kuma ya kamata Catalina ta yi?

Ya kamata David ya bayar da haƙuri ko kuma ya yi bayani abin da yake nufi. Ya kamata mahalarta taron su yi la'akari da yanda za a fahimtar ayyukansu daban a kan da abun da suke nufi, amma wannan ba yana nufin abin da wasu ke gani ba daidai ba ne.

• Idan fa Catalina ta tuntuɓi David ta intanet a maimakon ido da ido?

In da a ce Catalina ta fuskanci David a wani aiken da kowa da kowa zai gani, sauran mutanen za su iya aunawa matsalar sannan su yi bayani a kan wasan da ke ciki ko kuma dalilin da ya sa bayanin bai dace ba. Za a iya warware matsalar, ko kuma za ta iya girma a tsakanin sauran mutane. Idan Catalina ta haɗu da David ta hanyar sako a intanet, David zai iya tattauna matsalar tare da ita bayannan sannan ya gyara aiken shi idan ya gamsu cewa bai dace ba.

• Shin za ka iya tuna wani misalin irin wannan yanayin da ya faru a rayuwa?

Ya kamata a ga mahalarta taron a cikin yanda za a magance lamarin rashin ingancin sadarwar da aka yi a baya. Ka sanya a ranka cewa raba waɗannan misalan na zahiri a rayuwa zai iya kasancewa rashin samun natsuwa ga mahalarta taron. Ba su damar raba misalan abokai ko mutanen da suka sani (da. kansu).

• Idan fa Catalina ta fara kiransa mai cutarwa? Yaya kake ganin idan aka kalli mutum a matsayin mai zalunci zai shafi sunan David a nan gaba?

Ya kamata mahalarta taron su kasance a cikin abun da zalunci sannan su yi la'aƙari da yanda abubuwa a intanet za su iya shafar yanda sa'o'i ke ɗaukar ka.

## Labari na 3

Aditi tana kan dandalin sadatwar zamani a lokacin da ta lura cewa Mary, wata yarinya a makaranta, ta ɗauki hotonta sannan ta rubuta, “haha #menenebazaasanyaba” (yi ma suturarta dariya). Lallai, Aditi ta hassala sosai.

• Mene zai faru?

• Me Ya Kamata Mary Ta Yi? Me ya kamata Aditi ta yi?

Ya kamata Aditi ta fuskanci Mary game da abun da ta yi domin ta nuna mata cewa ta ji zafin abun. Haka kuma Aditi za ta iya kai ƙarar abun da Mary ta aikata ga dandalin sadarwar zamani da kuma ga babba mutum (misali., iyaye / mai bayar da kulawa / malami, ko mai gudanarwar makaranta).

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.